Citation: Fallou Ngom (PI), Jennifer Yanco, Mustapha Hashim Kurfi, Garba Zakari, Babacar Dieng, Daivi Rodima-Taylor, and Rebecca Shereikis. 2022. "A Poem in Honor of the Emir of Kano." http://sites.bu.edu/nehajami/the-four-languages/hausa/hausa-manuscripts/falke-2729-wakar-sarkin-kano/.

# **Waƙar Sarkin Kano**

Wa bi nastaʿīnu

Amīru Kano atana yauma sabtin

Atana Alimun

| | |
|---|---|
| Sarkinmu Abdullahi ya zo Asabat | Ya bar Kano ranar Alhamis ba shakka |
| Muna gaisuwa albarkacinka muke da | Murna mukai mun marhaban da zuwanka |
| Sarkin Musulmi ya wuce ya yi sabaqa | Mai gandu na bi duk ana dubinka |
| Wannan tawali'u ne da Allah yai maka | Ladabi ya baka da martabar kakanka |
| Ya Abdu ya ɗan Abdu me kyan Abdu kai | Ka kai fagen da ake bukatar saninka |
| Allah Yakaika Yamaida kai da farin ciki Birnin | Kano ta yi marhabin da zuwanka |
| Birni tana gorantaka tufar da kai | Allah Yakaika gidanka domin Makkah |
| Bana Ingilan ta yi arziƙi da ka je mata | Fa sarauniya ta tashi don girmanka |
| Manyan nasaran Britin da birninsu | Har jami'ansu da nufin zuwa kallonka |
| Wannan karama ce da Allah yai maka | Ya fawwala makhlūqāti duk sun bi ka |
| In khāliqi ya so mutum da farin ciki | Fa wurin halitta duk yake haɗa maka |